# Ba'a yi wa wani mutum bulala sama da goma sai a haddi daga cikin haddodin Allah

Daga Abu Burda - al-Ansari - Allah Ya yarda da shi - cewa shi ya ji Manzon Allah - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - yana cewa: "Ba'a yi wa wani mutum bulala sama da goma sai a haddi daga cikin haddodin Allah"

[Ingantacce ne] [Bukhari da Muslim ne suka rawaito shi]

Annabi - tsira da amincin Allah su tabbata agare shi - ya yi hani a yi wa wani bulala sama da bulala goma sai dai a cikin saɓo, ba wai ana nufin cewa abinda ya zo a cikinsa na iyakance adadi daga mai shara'antawa na bulala ko duka ko uƙuba keɓantacciya ba, abin nufi ba'a yin ƙari a cikin bulalar ladabtarwa akan bulala goma, kamar yi wa mata bulala ko ɗa.

http://www.sunnah.global/hadeeth/ha/show/2987